https://www.al-feqh.com/ha

# Talbiyya

## Talbiyya

Ita ce, faɗin Alhaji "Labbaikal Lahumma Labbaik, Labbaika La Sharika Laka Labbaik, Innal Hamda Wanni'imata Laka Wal Mulk, La Sharika Lak"

Saboda hadisin ɗan Umar – Allah ya yarda da shi – ya ce, Haka Manzon Allah (S.A.W) ya ke talbiyya.

Ma'anar «Labbaikal Lahumma Labbaik» (Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi) Shi ne na ansa maka, na ansa maka.

Talbiyya ta ƙunshi yabo da godiya ga Allah, na ansa wa umarninsa, da bayyana kaɗaitar shi, da kuɓuta daga shirka.

## Hukuncin Talbiyya

Yin talbiyya sunna ce, namiji zai ɗaga muryarsa da ita, mace kuwa zata yi ƙasa-ƙasa da muryarta, don gudun fitina.

## Lokacin Talbiyya Da Wuraren Da Ake Yin Ta

Maniyyaci zai fara talbiyya bayan sanya ihraminsa, ya yi ta yinta a kan hanyarsa. Ana ƙarfafa yin ta a wurare da yawa, daga cikinsu akwai :

Idan ya hau tudu, ko ya yi gangara, ko ya yi sallar farilla, ko idan dare ya yi, ko rana ta yi.

Zai daina yin talbiyyar umara idan ya ga ka'abah ya sumbaci Hajarul Aswad. A hajji kuwa zai daina talbiyya idan ya fara jifan wurin jifa na ƙarshe a ranar idi.



https://www.al-feqh.com/ha